# Surah 101: Al-Qari'ah - سورة القارعة

بسم الله الرحمن الرحيم

[101:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

ٱلۡقَارِعَةُ ١

[101:1] Abin sa gigicewa.

مَا ٱلۡقَارِعَةُ ٢

[101:2] Abin sa gigicewa kuwa na gaske!

وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ٣

[101:3] Ko ka san abin da ake nufi da abin sa gigicewa?

يَوۡمَ يَكُونُ ٱلنَّاسُ كَٱلۡفَرَاشِ ٱلۡمَبۡثُوثِ ٤

[101:4] Ranar da mutane za su fito kamar 'ya'yan fari masu watsuwa.

وَتَكُونُ ٱلۡجِبَالُ كَٱلۡعِهۡنِ ٱلۡمَنفُوشِ ٥

[101:5] Kuma tsaunuka za su kasance kamar wulin sufi.

فَأَمَّا مَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ٦

[101:6] Wanda ma'aunansa ya yi nauyi.

فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ٧

[101:7] To, shi yana a cikin wata rayuwa yardadda.

وَأَمَّا مَنْ خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ ٨

[101:8] Amma wanda ma'aunansa babu nauyi.

فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٌ ٩

[101:9] To, mazauninsa uwarsa Hawiya ce.

وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا هِيَهْ ١٠

[101:10] Ko ka san mece ce ita?

نَارٌ حَامِيَةٌۢ ١١

[101:11] Wata wuta ce mai zafi.